# Abun da kake bukatar sani game da cutar corona 2019 (COVID-19)

### Menene cutar corona 2019 (COVID-19)?

Cutar corona 2019 (COVID-19) wata rashin lafiyar numfashi ce wadda ke iya yaduwa daga wani mutum zuwa wani. Kwayar cutar da ke haddasa COVID-19 ita ce kwayar cutar corona wadda aka fara ganowa a lokacin wani binciken da aka gudanar kan barkewar wata annoba a birnin Wuhan na kasar Sin.

### Ko mutanen dake Amurka za su iya kamuwa da cutar COVID-19?

Cutar COVID-19 tana yaduwa ne daga wani mutum zuwa wani mutum a kasashe da dama, kuma an lura da bazuwar al'umma a cikin Amurka. Kasadar kamuwa da cutar ta ta'allaka ne kan mu'amala.
Mu'amalolin kusa da kusa na mutanen da suka kamu da cutar suna da matukar hadari, misali mu'amalar ma'aikatan lafiya da mutanen da suka kamu da cutar da ke haddasa COVID-19 na cigaba da nazartar halin da ake ciki sau da kafa.

### Ko an samu afkuwar cutar COVID-19 a Amurka?

E. An samu rahoton afkuwar cutar COVID-19 ta farko a Amurka a ranar 21 ga watan Janairun 2020. Kididdiga a halin da ake ciki kan afkuwar COVID-19 a Amurka ana iya samun ta a kan shafin yanar gizon CDC **https://www.cdc.gov/coronavirus/2019-ncov/cases-in-us.html.**

### Ya cutar COVID-19 ke yaduwa?

Kwayar cutar da ke haddasa COVID-19 meyiwuwa ta fito ne daga dabbobi, amma yanzu tana yaduwa daga wani mutum zuwa wani. Yana da muhimmanci a lura cewa yaduwa daga wani mutum zuwa wani mutum na iya faruwa ne a nahiya. Wasu cututtuka suna matukar yaduwa (kamar kyanda), yayinda sauran cututtuka suna da sauki a wurin yaduwa. A wannan lokacin, ba a san yanayin halin yaduwar kwayar cutar da ke haddasa COVID-19 a tsakanin mutane ba. Ka shiga shafin yanar gizon CDC don kara sani game da yaduwar sabuwar cutar corona da ta bulla **https://www.cdc.gov/coronavirus/ 2019-ncov/about/transmission.html.**

### Menene alamomin COVID-19?

Maras lafiya da ke dauke da cutar COVID-19 suna da rashin lafiyar numfashi mai sauki zuwa mai tsanani tare da alamomin

- zazzabi
- tari
- takaicewar numfashi

### Wace irin matsananciyar rikicewa ce ake samu daga wannan cutar?

Mafi yawancin maras lafiya suna da ciwon hakarkari a dukan huhunansu.

### Ya zan iya taimakawa wurin kare kai na?

Hanya mafi inganci ta samun kariya daga kamuwa ita ce kauce ma haduwa da kwayoyin cutar da ke haddasa cutar COVID-19.

### Akwai ayukkan samun kariya masu sauki na yau da kullum da za su taimaka wurin kariya daga yaduwar kwayoyin cutar numfashi. Wadannan sun hada da

- Ka guji mu'amalar kusa da kusa da mutanen da ba su da lafiya.
- Ka guji taba idanunka, da hancinka, da kuma bakinka da hannuwanka da ba ka wanke ba.
- Ka rika wanke hannuwanka akai-akai da sabulu da ruwa na tsawon lokaci akalla da kikoki 20. Ka yi amfani da sinadarin tsaftacewa hannu wanda ke dauke da akalla kashi 60 bisa dari na alcohol idan babu ruwa da sabulu..

### Idan ba ka da lafiya, don hana yaduwar cutar zuwa ga wasu, ya kamata ka

- Tsaya a gida a lokacin da ba ka da lafiya.
- Ka rufe bakinka da hancinka a lokacin da kake tari ko atishawa da takardar tsaftacewa, sannan ka jefa takardar acikin kwandon shara.
- Ka rika wankewa da kashe kwayoyin cuta akai-akai kan abubuwa da wuraren da ake yawan tabawa.

### Me ya kamata in yi idan na yi tafiya ba da dadewa ba zuwa wata kasa daga Amurka?

Idan ka fita Amurka a cikin kwanaki 14 da suka wuce kuma ka ji ba ka da lafiya tare da zazzabi, da tari, ko wahala wurin yin numfashi, ka nemi kulawar jami'an lafiya. Ka kira ofishin masu kula da lafiyarka kafin ka tafi, kuma ka ba su labarin tafiyar ka tare da alamomin da ke damun ka. Za su ba ka dokoki kan yadda za ka kula da kanka ba tare da ka yada ma sauran mutane rashin lafiyar ka ba. A lokacin da ba ka da lafiya, ka guji haduwa da mutane, kar ka fita waje kuma ka dakatar da duk wata tafiya don rage yiwuwar yada rashin lafiyar zuwa ga wasu.

### Ko akwai rigakafi?

A halin yanzu babu rigakafin kariya daga kamuwa da cutar COVID-19. Hanya mafi inganci ta samun kariya daga kamuwa ita ce a guji haduwa da kwayar cutar da ke haddasa COVID-19.

### Ko akwai maganin cutar?

Babu wani takamammen maganin cutar COVID-19. Mutanen da ke dauke da cutar COVID-19 na iya neman kulawar lafiya don taimakawa wurin rage radadin alamomin.

### Don karin bayani a ziyarci: www.cdc.gov/COVID19

Maris 2020

**A LURA:** Bayanai kan COVID-19 suna canzawa nan take kuma za a sabunta takardun bayanan kamar yadda ya kamata